# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da



# Sarakuna masu Kirki, Sarakuna marar Kirki

**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Lazarus**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**

**Ranar bakin ciki ne ga Mannase. Babansa, Sarki Hezekaiya ya mutu. Yanzu, shi shekarunsa goma sha biyu ne, kuma Mannase shi sabon sarki ne a kan mutanen Allah a Yahuda. Bai sani ba tukuna, amma Mannase zai yi mulki har shekaru 55. Mannase yana bukatan taimakon Allah domin ya zama sarki mai kirki.**



**Amma Mannase ya yashe Allah sai ya aikata mugunta. Mannase ya sake gina bagadai na sujadan gunki. Ya ma gyara wani siffa sai ya kafa shi a cikin Haikalin Allah! Allah ya riga ya gaya wa Musa, "Ba za ka yi wani siffa ko siffofi ba. Ba za ku bauta musu ko ku yi musu hidima ba."**



**Manase ya bi bokaye da duba. Ya bi da mutanen nesa da Allah. Sarkin ya ma kone ‘ya’yansa hadaya ga gumaka. Rashin biyayya na Mannase ya sa Allah fushi sosai.**



**Sa’ad da mutanensa suka yi masa rashin biyayya, Allah yakan bari a hukunta su.  Abin da ya faru da Mannase da mutanen da yake mulki a kansu.  UBANGIJI ya kawo sojojin Assiriyawa a kansu.  A ka dauke Mannase a sarkoki zuwa Babila.**





Wahala a Babila, Mannase ya roke UBANGIJI, Allahnsa.  Ya kaskantar da kansa sosai a gaban Allahn kakaninsa, ya yi addu’a a gareshi.  Ya hana yin addu’a ga matacen gumaka! Amma, Allah mai rai zai amsa addu’ar Mannase bayan duka mugayen abubuwan da ya yi?

**I’i!  Allah ya ji addu’ar sarki ya dawo da shi zuwa Urushalima, zuwa kursiyin, zuwa ga zaman sarki a bisan mutane.  Sai Mannase ya sani cewa UBANGIJI shi Allah ne.**



Sarki Mannase ya zama sabon mutum.  Ya fitar da sifar da ya yi daga haikalin Allah sai ya tattara allolin al’ummai a Urushalima.  Ya kawar da su duka.  Ya gyara bagaden UBANGIJI ya mika hadayan godiya.  Sai ya umarta mutanensa su yi wa UBANGIJI Allah na Isra’ila hidima.  Yanzu Mannase ya canja!



**Bayan da Mannase ya mutu, dansa, Amon, ya koma ga yin sujada ga gumaka. Amma bai kaskantar da kansa a gaban Ubangiji kamar Mannase ba. Yayinda Amon yana ta zunubi a kan zunubi, 'yan hidimarsa a karshe suka kashe shi, a cikin gidansa. Ya yi mulki shakara biyu kawai.**



Sarki na biye, Yosiya, shekarunsa takwas ne da ya zama sarki.  Ya yi mulki shekaru 31 kuma ya yi abin da ya dace ga Allah.  Ya hallakar da sujadan karya da duka allolin karya.  Gaskiya kam, Yosiya ya yi nika gumakan kurmus.





**Sarki Yosiya mai kirki ya kuma share ya gyara Haikalin Allah. A cikin kayan datti, wani firist ya sami Littafin Doka wanda UBANGIJI ya ba wa Musa.**





**Sa’ad da sarki ya ji kalmomin Dokar, sai yayyage rigunasa cikin bakin ciki.  Yosiya ya sani rin mugunta da kakaninsa suka yi ta wurin rashin biyayya ga Dokar Allah.**

Wata annabiya mai suna Hulda ta ba wa Yosiya sako daga wurin Allah. “In ji UBANGIJI, ‘Gashi, zan kawo duka la’antar da ke cikin littafi a kan wannan wuri saboda sun yashe Ni.’” Amma saboda Yosiya mai saukin kai ne da mai biyayya, wannan ba zai faru ba sai bayan mutuwarsa.



Allah ya taimaki Yosiya ya komar da mutanensa zuwa ga UBANGIJI. Wata rana, yayinda yake bi da sojoji zuwa yaki, sai aka ji ma Yosiya rauni mai tsanani da bakan abokin gaba. Masu yi masa hidima suka kai shi Urushalima da keken doki inda ya mutu. Duka mutanensa suka yi makokinsa suka kuma shirya wakoki game da Sarki Yosiya mai kirki.





**Ba a dadde ba sai mulkin ya kare. Amma wata rana, wani sarki zai yi mulkia bisan Isra'ila. Sunansa shi ne SARKIN SARAKUNA, DA ALLAHN ALLOLI. Sa'ad da Yesu Kiristi ya far zuwa, an ki shi aka kuma giciye shi. Sa'ad da Yesu Kiristi zai zo kuma, ba wai a kan Isra'ila ne kadai zai zama sarki kawai ba, amma kan dukan duniya ne.**

**Sarakuna masu Kirki, Sarakuna marar Kirki**

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**2 Tarihi 33-36**

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE

23

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**